**Hausa** **الهوسا**

# منزلة الصلاة في الإسلام

**المفهوم، والحكم، والمنزلة، والخصائص، وحكم الترك، والفضائل**

**في ضوء الكتاب والسنة**

**تأليف الفقير إلى الله تعالى:**

**د. سعيد على بن وهف القحطاني**

# MATSAYIN SALLAH A CIKIN MUSULUNCI

(Ma'anarta, Hukuncinta, Abubuwan da ta kebanta da su, Hukuncin wanda ya bar Sallah, da kuma falalolinta).

Dai dai da yadda suka zo a cikin Alkur'ani da Hadisa

Wallafar mabukaci zuwa ga Allah Madaukaki

Sa'id Bn Ali Bn Wahf Al-kahtani

IslamHouse.com

شركاء التنفيذ:

دار الإسلام جمعية الربوة رواد الترجمة المحتوى الإسلامي

يتاح طباعة هذا الإصدار ونشره بأي وسيلة مع الالتزام بالإشارة إلى المصدر وعدم التغيير في النص.

Telephone: +966114454900
ceo@rabwah.sa
P.O.BOX: 29465
RIYADH: 11557
www.islamhouse.com

بسم الله الرحمن الرحيم

# DA SUNAN ALLAH MAI RAHAMA MAI JINKAI

## Gabatarwa

Lallai Godiya ta tabbata ga Allah, Muna gode masa kuma muna neman taimakonsa, kuma muna neman gafararsa.Kuma Muna neman tsarin Allah daga Sharrin zukatanmu da Munanan AyyukanmuKuma Duk wanda Allah ya shirye shi to babu mai batar da shi, kuma duk wanda ya batar da shi to babu mai shiryar da shi, kuma na shaida babu wani abun bauta da gaskiya sai Allah shi kadai bashi da abokin tarayya, kuma na Shaida Annabi Muhammad Bawansa ne kuma Manzonsa ne, -Tsira da Amincin Allah su tabbata a gareshi da Alayansa da Sahabbansa, da duk wadanda suka bishi har zuwa Ranar alkiyama, kuma ka Amince su Amincewa Mai yawa. **Bayan haka**:

To wan nan Takaitacciyar Makala ce game da: **[Matsayin Sallah a Musulunci]**, Na bayyana a cikinta a takaice Ma'anar sallah da Hukuncin ta da Matsayinta, da Abun da ta kebanata da shi, da Hukuncin wanda ya Barta, da Falalarta, Cikin Dalilai daga Al-Qur'ani da Kuma Sunnah.

Kuma hakika na amfana da yawa da wasu Jawabai da Zabin Babban Malamin mu Abdu-Aziz Bn Abdullahi Bn Baz -Allah ya daga Darajojinsa cikin Aljannar Firdausi Madaukakiya.

Kuma ina rokon Allah ya Sanya wannan Karamin aikin Mai Albarka, kuma ya zamanto anyi shi don shi saboda Girman Allah, kuma ya anfanar da shi a Rayuwata da bayan Mutuwa ta, kuma ya anfanar da duk wanda yakai wurinsa; Don cewa Allah Mai tsarki shi ne Mafi Alkhairin wanda za'a roka, kuma Mafi Karamcin wanda za'a yi fata a gurinsa, kuma ya isar mana kuma madalla da wanda yake Mai lamuni, kuma babu tsumi babu dabara sai ga Allah Madaukaki kuma mai Girma, kuma tsira da Aminci su tabbata Ga Annabi -Tsira da Amincin Allah su tabbata a gareshi da Alayansa da Sahabbansa da kuma duk wanda ya bisu da kyautatawa har zuwa Ranar Alkiyama.

**Mawallafi**

**An rubuta a Safiyar Ranar Jumu'a**

**wanda yayi dai dai da 18/8/1420 Hijiriyya**

## **BABIN FARKO**: **MA'ANAR SALLAH**:

Sallah a Yaren Larabci: ita ce Addu'aAllah Madaukaki ya ce: “Ka Karbi Sadaka daga cikin Dukiyarsu zaka tsarkakesu kuma ka yabesu da ita kuma kayi musu Addu'a lallai cewa Addu'arka a garesu Nutsuwa ce a garesu, kuma Allah shi ne Mai ji kuma Masani”. (At-Tauba: 103). Ai kayi musu Addua, kuma Annabi Amincin Allah ya tabbata a gare shi ya ce: (Idan aka gayyaci Dayanku to ya amsa gayyata, to idan yana Azumi ne to yayi Addu'a, idan kuma bakinsa yana bude to ya ci). Ai yayi Addu'ar Albarka da Alkairi da Gafara.

Kuma Salati daga Allah shi ne kyakkyawan yabo, kuma daga Mala'iku Addu'a Allah Madaukaki ya ce: “Lallai Allah da Mala'ikunsa suna Salati ga Annabi ya ku wadan da kukai Imani kuyi masa Salati kuma kuyi masa Sallama Matukar Sallama” (Al-Ahzab: 56). Abul-Aliya ya ce: (Salatin Allah: shi ne yabonsa a wajen Mala'iku, Kuma Salatin Mala'iku: shi ne Addu'a). Kuma Ibn Abbas -Allah ya yarda da su- ya ce: (Suna yin Salati: ai suna Addu'ar Albarka).

Awata fadar kuma: Lallai cewa Salatin Allah shi ne Rahama, Salatin Mala'iku kuma Istighfari.

Kuma abun da yake dai-dai shi ne Maganar farko don Allah Madaukaki ya ce: "Wancananka sune wadanda suke da Salati daga Ubangijinsu da kuma Rahama kuma Wancananka su ne shiryayyu". (Al-Baqara: 157). Ai yabon Allah ya tabbata a gare su da kuma Rahamarsa, to sai ya jingina Rahama kan Salati kuma jinginawar yana nuna akwai banbanci a tsakaninsu.

To Salati daga Allah yana nufin yabo, daga kuma Halittunsa: Mala'iku, Mutane, Aljannu: yana nufin Ruku'u da Sujada, da Addu'a, da Tasbihi, Sallah kuma daga tsuntsaye da duk abu mai tashi tana nufin: Tasbihi.

**Sallah a Sharia**: ita ce Ibada ga Allah wacce take dauke da Maganganu da Ayyuka sanannu kuma kebantattu, wacce ake budeta da Kabbarar harama kuma ake rufeta da Sallama, kuma nkirawota da sunan sallah don ta kunshi Addu'a.

To Sallah ta kasance suna ga kowace Addu'a to sai ta zamanto Suna ne ga dukkan wata Addu'a ta Musamman, ko

kuma ta kasance suna ga wata Addu'a, sai aka dauketa zuwa ga Salla ta Shari'a saboda abun da yake tsakanin ta Addu'a na Dangantaka, kuma Umarni a cikin hakan yayi kusa kusa, idan aka kirawo sunan Salla a Shari'a to baza'a fahimci komai ba sai Sallar shari'a din to dukkanta Addu'a ce:

**Addu'ar Roko**: kuma wan nan ita ce Neman abun da wanda yake rokon yake nema na jawo Amfani, ko yaye wata cuta, kuma neman bukatu daga Allah yake shi kadai ta hanyar furta bukata a Harshe.

**Addu'ar Ibada**: kuma ita ce neman Ladan Allah da Ayyuka nagari: Na tsayuwa, da Ruku'u, da Sujada, to duk wanda yayi wadan nan abubuwan to hakika ya roki Ubangijinsa, kuma ya nema da harshensa na Hali cewa Allah ya gafarta masa, sai wannan ya bayyana cewa lallai sallah baki dayanta Addu'a ce ta Roko, kuma Addu'a Ibada ce; don ta kunshi hakan baki dayan sa.

# BABI NA BIYU: HUKUNCIN SALLAH

Sallah Wajibi ce: a cikin Qur'ani da Hadisi da Ijma'in Al'umma akan kowane Musulmi Baligi Mai Hankali, Sai dai Mai Haila kawai da Mai Jinin Biki, amma inda hakan yazo a Al-Qur'ani a fadin Allah Madaukakin sarki: "Bamu Umarce su sai don su bautawa Allah suna masu tsarkake Addini a gare shi Suna masu Bujirewa dukkan Bata kuma su tsaida Sallah kuma suna bada Zakka kuma wannan shi ne Addini Tsayayye". (Al-Bayyina: 5). Kuma Allah Madaukakin Sarki ya ce: "Lallai sallah ta Kasance akan Muminai Wajibine Mai lokaci". (An-Nisa: 103).

Amma Sunnah Kuma, saboda Hadisin Mu'az -Allah ya yarda da shi- lokacin da Annabi -Tsira da Amincin Allah yarda da shi- ya aikeshi zuwa Yeman kuma ya ce da shi: (Kuma ka Sanar da su cewa Allah ya Farlanta musu Salloli Biyar a kowace Rana; Safe da Maraice). Da kuma Hadisin Bn Umar -Allah ya yarda da su daga Annabi cewa ya ce: (An gina Musulunci akan Abubuwa Biyar: Shaidawa Babu abun bautawa da Gaskiya sai Allah, kuma cewa Annabi Muhammad Mazonsa ne, da kuma tsaida Sallah, da Bada

Zakkah, da azumtar Watan Ramadan, da Hajjatar Dakin Allah).

Daga Ubadata Dan Samit Allah ya yarda da shi- ya ce: na ji Manzon Allah Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi ya na cewa: ((Salloli Biyar Allah ya Wajabtasu akan Bayi, kuma Duk wanda yazo da su bai tozarta komai daga cikinsu ba Don tozartar da Hakkinsu, to Alkawarin Allah ya tabbata akansa cewa zai shigar da shi Al-jannah)). Hadisi

Kuma akwai Ayoyi da Hadisai Masu yawa sunzo cikin Farillar Sallah.

**Kuma a Ijma'i**, to Hakika Al-umma baki daya ta hadu akan wajabcin Salloli biyar a Dare da Rana.

Kuma bata wajaba akan Mai Haila ko mai Jinin biki saboda fadin Annabi Amincin Allah a gare shi y ace: ((A she idan Mace tayi Haila bata yin sallah kuma bata Azumi?)).

# BABU NA UKU: MATSAYIN SALLAH A CIKIN MUSULUNCI

Sallah tana da Matsayi Mai girma a cikin Musulunci kuma yana daga cikin abun da yake nuna Muhimmancin ta da girman Matsayinta wadan nan abubuwa masu zuwa:

1- **Sallah kuma ita ce ginshikin Addini** wanda baya tsayuwa sai da ita, a Hadisin Mu'az -Allah ya yarda da shi- Cewa Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi ya ce: ((Tushen Al-amari shi ne Musulunci, kuma Ginshikansa Sallah, kuma kololuwarsa shi ne Jahadi)). Kuma idan gishiki ya fadi to abunda aka gina akansa.

2- **Farkon abun da za'a fara yiwa bawa Hisabi akansa na ayyukansa**, to gyaruwar aikinsa da bacinsa duk yana hade ne da gyaruwar Sallarsa ko bacinta, daga Anas Bn Malik -Allah ya yarda da shi- daga Annabi -tsira da Amincin Allah su tabbata a gareshi ya ce: ((Farkon abun da za'ayiwa Bawa Hisabi akan sa a ranar Alkiyama shi Sallah, to idan ta gyaru to komai na

aikinsa ya gyaru, kuma idan ta baci to komai na aikin sa ya baci)). A cikin wata Riwaya: ((**Farkon abun da za'a tambayi bawa akan sa Ranar Alkiyama za'a fara bincika Sallarsa**, **to idan ta gyaru to hakika ya rabauta**, **[a cikin wata Riwayar kuma**: **kuma zai ci Nasara]**, **kuma idan ta baci to hakika ya tabe kuma yayi Hasara**)).

Kuma daga Tamim Al-dari -Allah ya yarda da shi- zuwa ga Annabi: ((Farkon abun da za'ayiwa Bawa Hisabi akansa a Ranar Alkiyama shi Sallarsa to idan ta kasance ya cika ta to sai a rubuta masa ita cikakkiya, kuma idan ya kasance bai cikata ba, Allah Madaukakin sarki zai ce da Mala'ikunsa: ku duba ko bawana ko zaku samu wani tadawwu'i to sai ku cika masa Farillarsa da shi, Sannan zakkah ma Haka, Sannan sai a dauki sauran Ayyukan irin hakan Ita ce)).

3- **Karshen abun da zaa rasa a Addini**, to idan karshen Addini ya tafi babu abun da zai yi Saura da cikin sa, daga Abu Umama Zuwa Annabi: ((Za'a rika warware Igiyoyin Addini Igiya bayan Igiya, kuma ko yaushe Igiya ta Warware sai Mutane su kama wata igiyar da take binta, Igiyar Farko ta warwarewa ita ce Hukunci,

kuma igiyar karshe ita ce Sallah)). cikin wata Riwayar Kuma ta wata Hanyar: ((Farkon abun da za'a daukewa Mutane Shi ne Amana, kuma na Karshen abunda zai wanzu shi ne Sallah, kuma da yawa Mai Sallah babu wani Alkairi a cikinsa)).

Daga Anas -Allah yarda da shi- daga Annabi: ((Farkon abunda zaku fara rasawa a Addininku shi ne Amana, kuma na Karshe shi ne Sallah)).

4- **Karshen Wasiyyar da Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi yayiwa Al'ummar sa**, daga Ummu Salama -Allah ya yarda da ita lallai cewa ta ce: Ya kasance karshen Wasiyyar da Manzon Allah yayi ita ce: ((Sallah da kuma abunda Hannunku ya Mallaka)). Har Saida Annabin Allah -Tsira da Amincin Allah su tabbata a gareshi yana Jinjina ta a Zuciyarsa kuma da abun da yake kwaranyowa daga harshen sa)).

5- **Allah ya yabi wadan da suka tsaya da ita kuma ya yi Umarni da ita**, to Sai Madaukakin sarki ya ce: "Kuma ka Ambaci Isma´ila a cikin Littafi. Lalle shi, ya kasance mai gaskiyar alkawari, kuma ya kasance

Manzo, Annabi. Kuma ya kasance yana umurnin mutanensa da Salla da Zakka. Kuma ya kasance yardajje a wurin Ubangijinsa". (Maryam: 54-55).

6- **Allah ya Zargi wadan da suke tozarta ta ko suke kiwar yinta**, Allah Madaukaki ya ce: "Sai wadansu ′yan baya suka maye a bayansu suka tozarta salla, kuma suka bi sha′awowinsu. To, da sannu za su hau da wani sharri". (Maryam: 59). Allah madaukakin sarki yace: "Lalle ne Munafukai suna yaudarhwa da Allah, alhali kuwa Shi ne mai yaudararsu; kuma idan sun tashi zuwa ga Sallah, sai su tashi suna masu kasala. Suna nunawa mutane, kuma ba su ambatar Allah sai kadan". (An-Nisa: 142).

7- **Mafi girman Rukunan Musulunci da ginshikansa Manya bayan kalmar Shahadu biyu**, Daga Abdullahi bn Umar -Allah ya yarda da su- daga Annabi -Tsira da Amincin Allah su tabbata a gareshi- ya ce: ((An gina Musulunci kan Abubuwa Biyar: Shaidawa Babu wani Ubangiji da ya cancanci a bauta masa da gaskiya sai Allah, kuma cewa Annabi Muhammad

Manzon Allah ne, da Tsaida Sallah da bada Zakkah, da Azumin Watan Ramadan, Da Hajjatar Dakin Allah)).

8- **Daga cikin abun da yake nuna Girman Al-amarinta** cewa Allah bai Farlantata ba a Kasa ta Hanyar Mala'ika Jibril, kawai ya farlantata ba tare da wani tsani ba kuma a Daren da akayi Isra'i a Sama ta Bakwai.

9- **An Farlantata Salloli Hamsin**, kuma wannan ya nuna Son da Allah yake yi mata, san nan Allah mai girma da daukaka ya Saukake ta ga bayin sa, sai ya Farlantata Salloli biyar a dare da Rana, kuma a matsayin Hamsin din ce a Ma'aunin lada, amma biyar a aiki, kuma wannan ya nuna girman Matsayinta.

10- **Kuma Allah ya bude Ayyukan wadan da suka rabauta da sallah kuma ya cikata da ita**, kuma wannan yana karfafa Muhimmancinta Allah Madaukakin sarki ya ce: "Lalle ne, Muminai sun sami Babban rabo. Wadanda suke a cikin sallarsu masu tawali´u ne.Kuma wadanda suke, sudaga barin yasassar magana, masu kau da kai ne. Kuma wadanda suke ga zakka masu aikatawa ne. Kuma wadanda suke ga

farjojinsu masu tsarewa ne. Face a kan matan aurensu, ko kuwa abin da hannayen damansu suka mallaka to lalle su ba wadanda ake zargi, ba, ne. Kuma duk wanda ya nemi wata hanya ta bayan wannan to wadan nan sune Masu keta Dokokin AllahKuma wadanda suke, suga amanoninsu da alkawarinsu masu tsarewa ne. Kuma da wadanda suke, su a kan sallolinsu suna tsarewa". (Al-Muminun: 1-9).

11- Allah ya Umarci Annabi Muhammad -Tsira da Amincin Allah su tabbat a gare shi- da Mabiyan sa kan cewa: "Su Umarci Iyalansu da ita, Allah Madaukaki ya ce: Kuma ka Umarci Iyalanka da yin sallah kuma kayi hakuri akanta bama Rokonka wani Arziki Mune ma masu Azurta ka kuma Karshen Makoma kyakkyawa ta Tabbata ga Masu jin tsoron Allah". (Taha: 132).

Kuma daga Abdullahi Dan Umar -Allah ya yarda da su- da Annabi cewa shi ya ce: ((Ku Umaci 'Yayanku da yin Sallah idan suka kai shekara bakwai, kuma ku dakesu akanta idan suka kai 'Yan shekara Goma, kuma ku raba musu wajen kwanciya)).

12- **An Umarci Mai Barci da Mai Mantuwa da su rama Sallah**, kuma wannan yana nuna Karfin Muhimmancin ta, daga Anas Bn Malik -Allah ya yarda da shi- daga Annabi -Tsira da Aminin Allah su tabbata a gareshi ya ce: ((Duk wanda ya Manta Sallah to ya Sallaceta idan ya tuna da ita, kuma babu wata Kaffara da zaiyi sai wannan)).

Kuma a cikin Riwayar Muslim: ((Duk wanda ya Manta da Sallah ko yayi bacci bai yi ta ba, to Kaffararta idan ya tuna ta to yayi ta)). Kuma an hada Mai Bacci da mai Farfadiya kwana uku ko kasa da haka, kuma hakika an rawaito hakan daga Ammar, da Imran Bn Husain, da Samsah Bn Jundub -Allah ya yarda da su-Amman idan ya Kasance Kwanakin sun wuce hakan to babu Ramuwa; Saboda wanda ya suma tsawon lokaci sama da kwana uku to yayi dai dai da Mahaukaci ta hanyar gushewar Hankalinsa, Kuma Allah shi ne mafi Sani.

# BABI NA HUDU: MUHIMMAN ABUBUWAN DA SALLAH TA KEBANTA DA SU A CIKIN MUSULUNCI

Sallah tana da Matsayi da ta kadaita da shi akan Sauran Ayyuka Managarta, daga cikinsu:

1- **Allah ya kirawo sallah da Imani** cikin fadinsa: "Kuma ba ya yiwuwa ga Allah Ya tozartar da imaninku, Lalle ne, Allah, ga mutane, hakika, Mai tausayi ne, Mai jin kai". (Al-Baqara: 143). Ai Sallarku zuwa Masallacin Kudus; domin Sallah tana gasgata aikinsa da kuma Fadinsa.
2- **Kuma ya kebance ta da Ambato Saboda banbance ta da sauran Wadansu Shari'un Musulunci** Allah Madaukakin Sarki ya ce: "Ka Karanta abun da akai Maka Wahayi na Littafin". (Al-Ankabut: 45). Kuma Karanta shi, shi ne bin shi da aiki da abun da ke cikinsa na baki dayan Shari'un Addini, sannan ya ce: "Kuma ka tsaida Sallah", To sai ya kebance ta da ambato don rarrabeta, kuma a fadinsa

Madaukaki: "Kuma munyi wahayi izuwa garesu na aikata Alkairai da kuma tsaida Sallah". (Al-Anbiya: 73)

Ya kebanceta da ambato tare da shigarta cikin baki dayan Alkairai, da wanin haka da yawa.

3- **An hadata a cikin Al-Qur'ani Maigirma da wasu da yawa daga cikin Ibadu**, daga cikin haka fadin Allah Madaukaki Sarki: "Kuma ku tsaida Sallah ku bada Zakkah kuma kuyi ruku'u tare da Masu ruku'i". (Al-Baqara: 43). Kuma ya ce: "To Kayi Sallah kuma ka soki abin layyar ka". (Al-Kausar: 2). Kuma ya ce: "Ka ce Lallai cewa Sallata da Ibada ta da rayuwa ta da kuma Mutuwa ta duk na Allah ne Ubangijin Talikai". (Al-An'am: 162). Kuma da wasu su Masu yawa.

4- **Allah ya Umarci Annabinsa -Tsira da Amincin Allah su tabbata a gareshi- cewa lallai ya Hakura akanta**, sai ya ce: "Ka umarci Iyalanka da yin Sallah kuma ka Daure kanta bama tambayarka wani arziki mu Muke Azurtaka". (Taha: 132). Tare da cewa shi -Tsira da Amincin Allah su tabbata a gareshi- An umarce shi da yin Hakuri akan baki dayan Ibadu; domin fadin

Allah Madaukaki ya ce: “Ka yi Hakuri kan Bautarsa”. (Maryam: 65).

5- **Allah ya Wajabtata cikin kowane hali**, Kuma ba'awa Mara lafiya Uzuri ba, ko wanda yake cikin tsoro, ko Matafiyi, waninsa; Kawai dai anyi Sauki ne a wani lokaci cikin Sharadanta, wani lokaci kuma a yawanta, kuma wani lokaci cikin ayyukanta kuma bata saraya Matuka akwai hankali.

6- **Allah ya shardanta ta a cikin mafi cikar Yanayi**: Na tsarki, Ado da kaya, da kuma fuskantar Alkibla abun da ba'a Shardanta ba a cikin Waninta.

7- **Kuma anyi amfani da baki dayan gabban Dan Adam a cikinta**: na zuciya, Harshe, da gabbai, kuma babu wata ibada da take da wannan.

8- **Kuma Anhana a shagalta da waninta**, har a darsawa a rai da lafazi da kuma Tunani.

9- **Kuma ita ce Addinin Allah wanda halittun da ke Sama da Kasa** suke Bautawa Allah da shi, kuma shi ne Mabudin shari'un Aannabawa, ba'a aiko wani Annabi ba sai an umarce shi da Sallah.

10- **An hada ta da gasgatawa a fadinsa**: "To bai gasgata ba kuma bai Sallah ba, Sai dai ya ya karyata kuma ya juya baya". (Al-Qiyama: 31-32). Kuma abubuwan da Sallah ta kebanta da su suna da yawa kwarai, ba kuma za'a hadasu da wasun su ba.

## BABI NA BIYAR:
## HUKUNCIN MAI BARIN SALLAH

Barin sallar farillah Kafirci ne, kuma duk wanda ya barta yana mai musuntata ya kafurta Kafirci Mafi girma wannan duka Ma'abotan ilimi sun hadu akan haka, kuma koda ya Sallaceta, Amma wanda ya barta baki daya, kuma yana kudurce da Wajabcinta kuma baya Musunta ta to shima ya Kafurta, kuma mafi Ingancin fadar malamai cewa Kafircin sa Babba ne kuma yana futar da shi daga Musulunci; Saboda dalilai masu yawa daga cikinsu a takaice wadan nan masu zuwa:

1) Allah Madaukaki ya ce: "Ranar da ake yaye Makyagyama kuma ana kiransu zuwa sujada amma basa iya waIdanusu suna cikin tsoro kuma kaskanci ya rufe su kuma hakika ana kiransu zuwa Sujada alhalin suna kalua". (Al-Qalam: 42-46). kuma wannan yana nuna cewa wanda yabar Sallah to yana tare da Kafirai da Munafukai wadan da bayansu zai wanzu kame idan Musulmai sukai Sujada, kuma da sun kasance cikin

Musulmi da anyi musi izini da yin sujada kamar yadda akai wa Musulmi Izinin.

2) Kuma Allah Madaukaki ya ce: “Ko wace rai tana jingine da abun da ta aikata, Sai Ma'abota hannun dama, Suna cikin aljannai suna ta Tambaya, Game da Mujrimai, Mai sakaku cikin Wutar Sakar, Suka ce bamu kasance cikin masu yin Sallah ba, Kuma bamu kasance ba cikin masu ciyar da Miskinai, Kuma Mun kasance muna kutsawa cikin masu kutsawa, Kuma mun kasance muna karyatawa da Ranar tashin alkiyama”. (Al-Mudassir: 38-46). To mai barin sallah yana cikin wadanda zasu shiga cikin Wutar sakar, kuma Allah Madauakaki yana cewa: “Lallai mujrimai suna cikin Bata da kuma Wuta, Kuma za'a rika Jansu a Fuskokin su cikin Wuta ana ce musu ku dandani Azabar Wutar sakar”. (Al-Qamar: 47-48).

3) Kuma Allah maigirma da Daukaka ya ce: “To idan suka tuba kuma suka tsaida Sallah kuma suka bada Zakka to sun zama Yan uwanku a Addini kuma Muna rarrabe Ayoyin ga mutane Masu sani”. (At-Tauba: 11). Sai ya Danganta Yan uwantakarsu ta Muminai da yin Sallah.

4) Daga Jabir –Allah ya yarda da shi– ya ce: Naji Manzon Allah tsira da Amincin Allah su tabbata a gareshi yana cewa: ((Tsakanin Mutum da Shirka da Kafirci shi ne barin Sallah)).
5) Kuma daga Abdullahi Bn Buraidah daga Babansa, ya ce: Manzon Allah –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gareshi ya ce: ((Alkawarin da yake tsakaninmun da su shi ne Sallah to duk wanda ya barta to ya Kafirta)).
6) Kuma daga Abdullahi Bn Shakik –Allah ya yarda da shi– ya ce: (Sahabban Annabi Muhammad –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gareshi– basa ganin wani abu na Ayyuka barinsa Kafirci ne ban da Sallah).
7) Kuma hakika Sahabbai duka sun hadu kan cewa Mai barin Sallah Kafiri ne kuma ba daya bane daga cikin Malamai ya fadi hakan ba.
8) Kuma Ibn Taimaiyya ya fada cewa Mai barin Sallah ya kafirta Babban Kafirci Saboda abubuwa goma.
9) Kuma Ibn Al-Kayyim –Allah ya yarda da shi– ya kawo Sama da Dalilai Ashirin da Biyu akan Kafircin wanda ya bar sallah kuma cewa Babban Kafirci.

Kuma abun da yake dai dai wanda babu kokwanto a cikinsa shi ne, cewa Mai Barin Sallah kai tsaye ya kafirta saboda wadan nan Dalilai Bayayyanannu.

10-Imam Ibn Al-kayyim -Allah yayi masa rahama ya ce: (Kuma hakika ya kafa Dalilin Kafircin wanda ya bar Sallah da Alkur'ani da Kuma Sunna, da Ijimai'n Sahabbai).

## BABI NA SHIDA: FALALAR SALLAH

1- **Tana hana Alfasha da kuma Munanan Ayyuka;** Allah Madaukakin sarki ya ce: "Ka karanta abunda abunda akai maka wahayi kuma ka tsaida Sallah Lallai cewa Sallah tana hana Alfasha da Mummunan Aiki, kuma Ambaton Allah shi ne Mafi Girma kuma Allah yana sanin abunda kuke aikatawa". (Al-Ankabut: 45).

2- **Kuma Mafifitan Ayyuka Bayan Kalmar Shahadu Biyu;** Saboda Hadisin Abdullahi Bn Mas'ud -Allah ya yarda da shi- ya ce: na tambayi Manzon Allah -Tsira da Amincin Allah su tabbata a gareshi- Wane aiki ne yafi kowanne? ya ce: ((**Sallah akan lokacinta**)) ya ce: sai na ce: Sai kuma me? ya ce: ((**Bin iyaye**)) ya ce: Sai kuma me? ya ce: ((**Jihadi a tafarkin Allah**)).

3- **Tana kankare Zunubai;** Saboda Hadisin Jabir -Allah ya yarda da shi- ya ce: Manzon Allah -Tsira da Amincin Allah su tabbata a gareshi- ya ce: ((**Kwatan kwacin Sallolin nan Biyar Kamar Korama ce a kofar gidan dayanku yana wanka a cikin ta sau biyar a Rana**)).

4- **Tana Kankare Zunubai;** Saboda Hadisin Abu Huraira -Allah ya yarda da shi- -Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce: ((Salloli Biyar, Haka Jumu'a zuwa Jumu'a, Da Azumi zuwa wani Azumin Suna Kankare Zunuban dake Tsakaninsu, Matukar an nisanci Manyan Zunubai)).

5- **Haske ce ga Ma'abocinta a Duniya da Lahira;** Saboda Hadisin Abdullahi Bn Umar -Allah ya yarda da su- daga Annabi -Tsira da Amincin Allah su tabbata a gareshi yana cewa ya Ambaci Sallah wata Rana ya ce: ((**Duk wanda ya kiyaye ta zata kasance Haske da Hujja a gareshi a Ranar Alkiyama**, **kuma duk wanda bai kiyaye ta ba bashi da wani Haske**, **ko Hujja ko Rabauta**, **kuma ya Kasance Ranar Alkiyama yana tare da Karun da Fir'auna da Hamana**, **da Ubayyu bn Khalaf**)). A cikin wani Hadisin na Abu Malik Al-Ash'ari -Allah ya yarda da shi-: ((**Sallah Haske ce**)), Kuma Saboda Hadisin Buraida - Allah ya Yarda da shi- daga Annabi -Tsira da Amincin Allah su tabbata a gareshi- cewa ya ce: ((**Kayi Bushara ga Masu tafiya Masallaci cikin Duhu da cikakken Haske a Ranar Alkiyama**)).

6- **Kuma Allah yana daukaka Darajoji da ita, kuma za'a kankare masa kusakurensa;** saboda Hadisin Thauban Baron Manzon Allah -Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- daga Annabi -Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- cewa lallai ya ce da shi: ((**Na horeka da yawaita Sujada, to cewa ba zakayi sujada daya ga Allah ba sai Allah ya daga darajarka da ita, kuma ya kankare maka Zunubinka da ita**)).

7- **Daga cikin ma-fi girman Hanyoyin shiga Aljanna tare da Annabi** -Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- Saboda Hadisin Rabi'ah Bn Ka'ab Al-Aslami -Allah ya yarda da shi- ya ce: ((Na kasance kwana tare da Manzon Allah -Tsira da Amincin Allah su tabbata a gareshi- sai na zo masa da Ruwan Alwala da kuma Bukatarsa sai ya ce da ni: ((**Roki**)), sai na ce: Ina rokonka Makwantakarka a cikin Aljanna, ya ce: ((**fadi wani abu dai?**)) sai na ce: wannan ni dai nake bukata, ya ce: ((**to ka taimakamun akanka da yawaita Sujada**)).

8- **Kuma tafiya zuwa Sallah ana rubuta ladaddaki da ita kuma sai an daga Darajoji Sannan kuma a kankare zunubai;** Saboda Hadisin Abu Hurara -Allah

ya yarda da shi- ya ce: Manzon Allah -Tsira da Amincin Allah su tabbata a gareshi- ya ce: ((Duk wanda yayi Alwala a Gidan sa, sannan kuma ya tafi zuwa Daki daga cikin Dakunan Allah; don ya sauke wata Farillah daga cikin Farillan Allah sai sawayensa biyu sun kasance daya a kankare masa Zunubin sa, dayan kuma a daga Darajarsa)).

Kuma a cikin wani Hadisin: ((**Idan dayanku yayi Alwala kuma ya kyautata Alwalar**, **Sannan ya futa zuwa Masallaci**, **ba zai daga Kafar Damansa ba Sai Allah ya rubuta masa lada da ita**, **kuma bai daga kafarsa ta hagu ba sai Allah Madaukaki ya kankare masa zubin sa da ita**)).

9- **Za'a shirya wata liyafa a cikin Aljanna da ita ko yaushe Musulmi** yayi jijjifi ko yayi yammaci: Saboda Hadisin Abu Huraira -Allah ya yarda da shi- daga Annabi --Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi: ((**Duk wanda Yayi jijjifi Zuwa Masallaci ko yayi yammaci**, **to sai Allah ya tanadar masa a cikin Aljannah wata Liyafa ko yaushe yayi Sammakon ko yayi yammacin**)). Kuma Liyafa shi ne abun da ake tanadarwa Bako saboda zuwansa.

10– **Allah yana gafarta zunubai da ita cikin abun da yake tsakanin sa da tsakanin sallar da ke binta;** Saboda Hadisin Usaman –Allah ya yarda da shi– ya ce: naji Manzon Allah –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gareshi yana cewa: ((**Mutum Musulmi ba zai yi Alwala ba kuma ya kyautata Alwalar**, **sannan ya sallaci wata Sallah sai Allah ya gafarta Masa abinda yake tsakanin zuwan wata Sallar da wannan Sallar**)).

11– **Kuma tana Kankare Zunubai;** Saboda Hadisin Usman –Allah ya yarda da shi– ya ce: Naji Manzon Allah ––Tsira da Amincin Allah su tabbata a gareshi– yana cewa: ((**Babu wani Mutum Musulmi da lokacin Sallar Farilla zai Riske shi**, **sai ya kyautata Alwalarta**, **da Khusu'inta**, **da Ruku'inta**, **sai ta kasance Kaffara ce ga abun da ya gabata na Zunubai**, **Matukar dai bai aikata Alkabira ba**, **kuSma wannan haka zai ta gudana a zamani baki daya**)).

12– **Kuma Mala'iku suna yin Addu'a ga maiyin ta Matukar yana zaune a wurin Sallar tasa**, kuma yana cikin Sallah Matukar dai Sallah ce ta tsare shi; Saboda Hadisin Abu Huraira –Allah ya yarda da shi– ya

ce: Manzon Allah -Tsira da Amincin Allah su tabbata a gareshi- ya ce: ((**Sallar Mutum a Jam'i tafi sallar Mutum daya a Gidan sa da Kasuwar sa da Lada Ashirin da bakwai**, **kuma cewa Dayan ku da zaiyi Alwala kuma ya kyautata Alwalar sa sannan ya tafi Masallaci**, **babu abunda ya futar da shi sai salla**, **kuma baya bukatar komai sai sallar**, **to ba zai taba wani taku daya ba sai Allah ya daga Darajarsa da ita**, **kuma a kankare masa Zunuban sa da ita har sai ya shiga Masallaci**, **to idan ya shiga Masallaci ya kasance cikin Sallah Matukar dai salla ce ta tsaida shi**, , **kuma Mala'iku zasu rika yi Masa Addu'a Matukar dayanku yana wurin Zaman sa wanda yayi Sallah a cikinsa**, **kuma suna cewa Allah kaji Kansa**, **Allah ka gafarta Masa**, **Allah ka karbi tubansa**, **Matukar bai cutar da wani a cikinsa**)).

**13-** Jiranta Zaman Dako ne a Tafarkin Allah' Saboda Hadisin Abu Huraira -Allah ya yarda da shi- cewa Annabi -Tsira da Amincin Allah su tabbata a gareshi- ya ce: ((**Bana shiryar da ku ba abun da Allah yake kankare zunubai da shi kuma ya daga darajoji?**)), suka ce: Eh Ya manzon Allah, sai ya ce: ((**Maimaita Alwala a lokacin da take Wahala**, **da yawan Tattaki zuwa Masallatai**, **da Jiran**

**Sallah bayan wata Sallar, to wannan shi zaman dako, to wannan shi ne zaman Dako**)).

14- **Ladan wanda ya futa zuwa Sallah ka mar ladan wanda yayi Harama da Hajji ne;** Saboda Hadisin Abu Umama -Allah ya yarda da shi- cewa: Annabi -Tsira da Amincin Allah su tabbata a gareshi- ya ce: ((**Duk wanda ya futa daga Gidan sa yana mai Alwala don yin Sallar Farilla**, **to Ladansa kamar Ladan wanda yayi Harama da Hajji'; kuma duk wanda ya futa zuwa Tasbihin Walaha babu abunda ya tsare shi sai ita**, **to Ladansa Kamar Ladan Wanda yayi Umra**, **kuma Sallah bayan wata Sallar wacce babu wani wasa a tsakaninsu Lada ne a can cikin Madaukaka**)).

15- Duk wanda ya Makara kuma yana cikin masu halartar ta to yana da Ladan wanda ya Halarta; saboda Hadisan Abu Huraira -Allah ya yarda da shi- ya ce: Annabi tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi: ((**Duk wanda yayi Alwala kuma ya kyautata Alwala**, **Sannnan yayi Jijjifi sai ya samu Mutane sun riga sunyi Sallah**, **to Allah zai bashi Ladan sa kwatankwacin Ladan wanda ya Sallace ta**, **kamar Wanda ya Risketa**, **kuma ba za'a tauye masa Ladan komai ba**)).

16– **Idan yayi Alwala kuma ya futa zuwa Sallah to yana cikin Sallah har sai ya dawo**, kuma za'a rubuta masa ladan Tafiyarsa da dawowarsa, saboda Hadisin Abu Huraira –Allah ya yarda da shi– ya ce: Manzon Allah –Tsira da Amincin Allah ya tabbata a gare shi ya ce: ((**Idan Dayanku yai Alwala a cikin gidansa**, **sannan yazo Masallaci**, **ya kasance cikin sallah har sai ya koma**, **to kada yace haka**)), Kuma ya hada tsakanin Yan yatsunsa. kuma daga shi dai –Allah ya yarda da shi– zuwa ga Annabi: ((**Daga lokacin da Dayanku zai futa daga Gidansa zuwa Masallacina**, **to kafarsa daya za'a rika Rubuta Masa lada dayar kuma za'a rika Kankare masa Zunubai har sai ya dawo gida**)).

Kuma Karshen Addu'armu ita ce Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin Talikai, kuma Tsira da Aminci su tabbata ga Annabinmu Muhammad da Alayansa da Sahabbansa da duk wadan da suka bishi har zuwa Ranar tasahin Alkiyama.

## ABUBUWAN DA KE CIKIN LITTAFIN

MATSAYIN SALLAH A CIKIN MUSULUNCI ............ 1

Gabatarwa ............ 4

Babin Farko: Ma'anar Sallah ............ 6

BABI NA BIYU: HUKUNCIN SALLAH ............ 9

Babu na Uku: Matsayin Sallah a cikin Musulunci ............ 11

Babi na Hudu: Muhimman abubuwan da Sallah ta kebanta da su a cikin Musulunci ............ 18

Babi na Biyar: Hukuncin Mai Barin Sallah ............ 22

Babi na shida: Falalar sallah ............ 26

الحمد لله رب العالمين